# Kyakkyawar Dangantaka a Intanet

Mahalarta taron za su bincika wasu halayen da ke haifar da kyakkyawa da nagartacciyar dangantaka, da kuma yanda wasu ɗabi'u a intanet ke taka rawa a kan kyakkyawar dangantaka da kuma dangantaka mara kyau. Haka kuma mahalarta taron za su bincika damar da kuma ƙalubalen da tsakanin dandalin sadarwar zamani da dangantakar da ke tsakanin sa'o'insu da koyon yanda ake inganta abubuwa a tsakanin sa'o'insu.

# Furta Kalmar Dangantaka

## Kashi na Ɗaya

**Tattaunawa a Aji**

Tattara mahalarta taron a da’ira.

**Sanar da Ɗalibanka**

Yau, Ina so in yi magana a kan yanda abun da muke yi a intanet ke da tasiri a kan kyakkyawar dangantakarmu. Haka kuma za mu yi magana game da abun da za ka iya yi domin ka “tsaya” ma wasu da kuma gano lokacin da abokanmu ke buƙatar taimako ga wasu matsalolinsu a dangantakar.

**Tambayi Ɗalibanka**

Wa ya ji labarin kalmomin “ƙin tsayawa” ko “tsayawa” Me waɗannan kalmomin ke nufi a gare ka?

**Tattaunawa a Aji**

Saurari amsoshi da aka bayar 2-3.

**Sanar da Ɗalibanka**

Kamar yanda ka bayar da shawara, mai sa ido shi ne wanda ya lura da wasu abubuwan da suka faru. A batunmu na yau, muna yin magana game da al’amuran da suka shafi dangantaka mara kyau/dangantaka mara nagarta. Mai tsayawa shi ne wanda yake yin wani abu don tsaya ma wani — wataƙila ta hanyar goyon bayan wanda lamarin ya shafa, ta hanyar taimakawa wajen tsayar da abubuwan, ko ta wasu hanyoyin, wanda ya danganci yanayin.

## Kashi Na Biyu

**Sanar da Ɗalibanka**

Yanzu bari mu yi magana game da dangantakar: farko, ya kamata mu gane cewa “dangantaka” wata kyakkyawar kalma ce. Saboda dalilanmu, za mu bayyana ma’anar “dangantaka” a matsayin duk wani haɗi tsakanin tsara. Misali, za a iya haɗa da tsaranka a matsayin abokai, abokin karatu, ko a matsayin mambobin ayyukan wajen-makaranta ɗaya (misali., kulob ɗin fim). Duk lokacin da muka yi magana a kan kyakkyawar dangantaka, ana samun wata tambaya mai wahala: “Mene ne ainihin abin da ake nufi da kyakkyawar dangantaka?” Kowane mutum yana da ra'ayoyi daban game da wannan batu, kuma akwai amsoshi da yawa masu kyau.

Domin tabbatar da cewa dukkanninmu muna kan shafi guda, mu yi tunani game da kalmomin da za su fayyace kyakkyawar dangantaka — abota, abokin karatu, wani nau'in dangantaka! Mun san cewa wasu lokutan abubuwa za su iya kasancewa ba daidai ba a kowace irin dangantaka, saboda haka bari mu yi magana a kan kyawawan ɗabi'u na musamman ga nau'o'i daban-daban.

Bari mu buga wani ƙaramin wasa. Kamar yanda muke zagaye da'ira, kowa ya faɗi kalma guda da za ta fayyace kyakkyawar dangantaka. Zan fara. Ina ganin dangantaka za ta iya zama _________________ (goyon bayan, kulawa, kirki, da dai sauransu).

**Tattaunawa a Aji**

Rubuta abun da mahalarta taron ke faɗi a kan flipchart.

**Sanar da Ɗalibanka**

Da kyau! Mun gode da ka bayar da gudunmawa! Bari mu duba waGɗannan kalmomin.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin mun amince da su?

Shin kana da wani abun da za ka ƙara?

Bisa ga waɗannan kalmomin, shin wani zai iya samar da wata jimla guda ɗaya da za ta iya fayyace ma'anar kyakkyawar dangantaka?

Jagoranci ƙungiyar wajen samar da ma'anar kyakkyawar dangantaka da za a iya rabawa.

# Gallari Walk

## Kashi Na Ɗaya

**Tattaunawa a Aji**

Raba mahalarta taro bibbiyu

**Sanar da Ɗalibanka**

Yanzu da muke da wani kyakkyawan jerin suna dangane da abubuwan da muke tunani a lokacin da muka yin magana game da 'kyakkyawar dangantaka,' lokaci ya yi da za mu juya akalarmu sannan mu duba tamu ƙwarewar tare da dangataka a kan intanet.

**Tattaunawa a Aji**

Rubuta wata tambaya guda ɗaya daga cikin jerin tambayoyin da ake da su a ƙasa a kan kwalin sanarwa sannan ka maƙala kwalin sanarwar a ɗakin.

Tambayoyin da Za a Iya Yi a Kan Kwalin Sanarwa:

1. Wane ne kake hulɗa da shi ta hanyar fasaha?

2. Wane dandalin sadarwa, ayyuka, ko shafukan yanar gizo kake yin amfani da shi wajen yin hulɗa da mutane?

3. Ta yaya intanet da fasahar wayar tafi-da-gidanka (kamar ƙaramar kwamfuta ko wayoyin tafi-da-gidanka) suka ba ka damar ƙirƙira ko kula da kyakkyawar dangantaka?

4. Ta yaya za ka kasance da mutanen da ke godiya ga na'urorin wayar tafi-da-gidanka da kwamfutoci?

5. Wasu ƙalubale ne ke tattare da intanet da fasahar wayar tafi-da-gidanka a wajen ƙirƙira/kulawa da kyakkyawar dangantaka?

6. Wace irin abota ce ka gani ko ka fuskanta saboda wasu abubuwan da ka aike da su a intanet?

**Sanar da Ɗalibanka**

Zan ba kowane mutum bibbiyu wasu takardun rubutu da alƙalami. A kan kwalin sanarwar a ɗakin akwai tambayoyi daban-daban. A yayin da na ba ka takardarka, za ka iya komawa ga kwalayen sanarwar. Rubuta amsarka a kan takardun rubutun

sannan ka sanya su a kan kwalayen sanarwar. Idan kana da amsa fiye da guda ɗaya ga tambaya, rubuta kowace amsa a takarda daban sannan ka sanya su a kan kwalayen sanarwar. Za a ba ka mintuna 8. Ji daɗi!

**Tattaunawa a Aji**

Karɓi kwalayen sanarwar a ƙarshen ayyukan sannan ka sake tattara ƙungiyar wuri guda.

**Tambayi Ɗalibanka**

Wasu amsoshi ne suka kasance bai ɗaya ga waɗannan tambayoyin?

Shin akwai wasu abubuwan da kake ganin an rasa?

Shin akwai wani abun da ake ya yi wanda ka lura da shi?

Ta yaya fasaha ta canza dangantakarka da abokanka?

Shin fasaha ta sauƙaƙa abubuwa ko kuma sun ƙara yin wahala? Me yasa?

# Tattauna Labarin

## Tattaunawa

**Sanar da Ɗalibanka**

Yanzu za mu tattauna a kan wani labarin da aka haɗa shi da fasaha da dangantaka wadda ake kira “over-texting.”

Shin akwai wanda ya san ma’anar “over-texting.”?

**Tattaunawa a Aji**

Saurari amsoshi da aka bayar 2-3.

**Sanar da Ɗalibanka**

Over-texting shi ne lokacin da wani ya aika da saƙonni da yawa ga wani mutumin wanda wannan mutumin ya ji ƙarfi.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin wani ta taɓa fuskantar over-texting?

Idan kai ne kake samun saƙon, me za ka yi? Me yasa?

Idan ɗaya daga cikin abokanka ya same sannan ya ce maka yana fuskantar irin wannan halin, wace shawara za ka ba shi? Shin za ka ɗauki mataki? Wasu irin matakai daban-daban za ka ɗauka?

1. Bi sawu: Ɗaukar waɗannan matakin domin taimaka ma abokinka shi ma ana kiransa da “tsayawa.”

**Tambayi Ɗalibanka**

Mene ne zai tsayar da wani daga tsaya ma abokin shi?

Bari mu yi kamar ɗaya daga cikin abokinka ya nemi abikinsu da su daina aiko masa da saƙonni da yawa. Me zai faru idan abokansu suka fara zuwa gidansu a kowane lokaci, suna neman ganinsu a kowane lokaci? Matsalar za ta iya yin muni, wadda za a iya kira da “tsananta.” Wace shawara za ka iya ba abokinka idan matsalar ta tsananta?

Idan matsalar ta tsananta, shin za ka iya bayar da amsa a matsayin wanda ya tsaya masa kamar da? Wane mataki za ka ɗauka yanzu domin zama wanda zai tsaya

masa?

**Sanar da Ɗalibanka**

“Over-texting” shi ne misali guda ɗaya kawai ga yanayin a inda fasaha za ta iya samar da kyakkyawar dangantaka.

**Tambayi Ɗalibanka**

Mene ne sauran misalan?

Wasu hanyoyi ne za su magance waɗannan matsalolin?

Mene ne tattaunawar da muka yi zuwa yanzu ta sanar da mu game da rawar da fasaha za ta taka a cikin dangantaka?

**Tattaunawa a Aji**

Jagoranci wata tattaunawa game da tasirin yiwuwa ko kuma rashin tasirin fasaha a cikin dangantaka.

# Ma’aunin Ayyuka

## Kashi Na Ɗaya

### Sanar da Ɗalibanka

Bari mu duba wasu ƙayyadaddun halaye a cikin kyakkyawar dangantaka ko dangantaka mara kyau da kuma inda suka faɗo a kan ma’auni daga kyakkyawa dangantaka zuwa dangantaka mara kyau.

Ina so in ba kowannen ku takardar rubutu. A kan takardar rubutun akwai wasu ayyukan da ke faruwa a cikin dangantaka, kamar “aika ma abokin zamanka saƙo na 24/7” ko “musayar kalmar sirrin dandalin sadarwar zamani.” Da zarar na baka takardar rubutu, ina so ka miƙe tsaye sannan ka zo gaban ɗakin. A gefe guda na ɗakin akwai mafi kyawon halayyar dangantaka, sannan kuma a gefe guda akwai mafi mumin halayyar dangantaka.

A lokacin da ka taso, ka yi tunani game da kyawo ko rashin kyawon halayyar a kan katin, sannan ka tsaya a cikin layi. Misali, idan ka yi imani cewa “aikawa da saƙo na tsawon 24/7” ba shi da kyau sosai sannan “so da kuma sake-raba duk wasu abobuwan da abokanka suka aike da su,” tsaya kusa da gefen mara kyau.

### Tattaunawa a Aji

Batutuwan katin da aka bayar da shawara:

1. Aika ma abokiyar zamanka saƙo 24/7
2. Musayar kalmar sirrin dandalin sadarwar zamani
3. Karanta saƙonnin kar ta kwanan abokinka ba tare da izinin shi ba
4. Yin magana da baƙo / mutanen da ba ka sani ba sosai a intanet
5. Aikewa da jawaban rashin ladabi a kan aiken dandalin sadarwar zamanin wani
6. Aikawa da saƙon “sai da safe” ko “ina kwana” (wataƙila kowace rana) ga wani wanda ka damu da shi
7. Yin magana game da wata jayayya da kuka yi da wani aboki a bayyane a dandalin sadarwar zamani
8. So da kuma sake-raba duk wani abun da abokanka suka aike da su
9. Aikewa da wansu abubuwa a dandalin sadarwar zamani ta hanyar yin amfani da asusun abokinka (a cikin sunansu)

10. Maƙala abokanka a cikin hotuna daga wani fati

11. Yaɗa gulma game da abokin karatunka a dandalin sadarwar zamani

A matsayin mahalarta taron da suka fito sannan kuma suka shirya kansu, tambaye su game da dalilin da yasa suke tsaye a wurin da suke, sannan ka ƙarfafawa mahalarta taron guiwar su matsa idan suna jin cewa suna buƙata.

Da zarar mahalarta taron sun shirya kansu zuwa wani ma'unin. nemi su sanya takardar karatun a jikin bango a gaban ɗakin sannan ka matsa baya saboda su iya ganin ma'aunin gaba ɗayansa.

**Tattaunawa a Aji**

Idan sun zaɓi yin hakan, mahalarta taron za su iya amsa tambayoyi guda biyu na farko a ƙasa ta hanyar wata tattaunawa, da rubuta su a takardar karatun da kuma sanya su a kan bangon a gaban ɗakin.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin akwai wasu halayya marasa kyaun da za ka iya yin tunani a kai?

Shin akwai wasu halayya madu kyaun da za ka iya yin tunani a kai?

Shin akwai wani tsari mai kyau ga wannan ma'aunin? Me yasa / me zai hana? Shin dukkanku kun yarda?

**Tambayi Ɗalibanka**

Mun sanya waɗannan ƙayyadaddun halayen a kan wani ma'auni daga kyakkyawar dangantaka zuwa dangantaka mara kyau. Amma, akwai yanda za a magance matsalar yayin da kyakkyawar halayya ta koma halayya mara kyau? Ko halayya mara kyau ta koma mai kyau? Yaushe ne hakan za ta faru?

Idan X halayya ce mara kyau [zaɓi wata ƙayyadaddiyar halayya da mahalarta taron za su kasance kusa da 'halayya mara kyau' a gefen ma'aunin], me za ka yi wajen magance matsalar?

Ta yaya za ka yi magana da wani ida ba ka gamsu da abun da suke yi ba?

# Aiki

## Kashi Na Ɗaya

### Sanar da Ɗalibanka

Mun yi magana da yawa yau game da fasaha da dangantaka. Yanzu da muka sa ka yi tunani, ta yaya za ka raba abun da koya tare da wasu? Wasu irin ayyuka za ka iya ƙirƙira domin ka ƙarfafawa sa'o'inka su zama masu tsaya ma wani idan sun fuskanci wani hali mara kyau a cikin dangantaka?

### Aiki

Rarraba mahalarta taron zuwa ƙungiyoyi masu mutane 3 ko 4.

### Sanar da Ɗalibanka

Muna da shawarwari guda biyu a halin yanzu, amma idan kana da wani ra'ayin daban, ka bayyana shi! Kana da mintuna 30.

1. Shawara #1: Samar da jerin abubuwan da za a gudanar a sha'anin saboda mambobin makarantarka ko al'ummun da ke kewaye da rawar da fasaha ke takawa a dangantaka. Wannan sha'anin zai iya kasancewa wani shirin da za a nuna/ tattauna, wayar da kawunan mutane "Yaɗa Makon Saytayya," ko ma gabatarwa! Samar da misalan yanda za ka yi amfani da dandalin sadarwar zamani, kamar Facebook ko Twitter, don tallata sha'anin. Saki jiki ka ƙirƙiri wasu abubuwan da za a nuna a intanet (misali., zane-zane, meme, da dai sauransu.).

2. Shawara #2: Ƙirƙiri wani labari game da wata dangantaka (misali., dangantaka tsakanin 'yan uwa, ko dangantaka a tsakanin abokai a makaranta) da yanda za ta shafi dandalin sadarwar zamani. Za ka iya samar da wani ɗan gajerin wasa, ƙirƙiri hoto (misali., zane-zanen ban dariya), ko ka rubuta wani bayanin tattauna a ɓangaren labaran Facebook ko Twitter . . . zama mai fasaha!

## Kashi Na Biya

### Aiki

Bayan mintuna 30 sun cika, nemi ƙungiyoyin su raba abubuwan da suka ƙirƙira sannan ka nemi su tattauna tambayoyin da ke ƙasa.

### Tambayi Ɗalibanka

Wane batu kake gabatarwa? Me kake so mutane su koya daga cikin ra'ayinka

Ta yaya wannan ra’ayin zai taimaki makarantarka/al’umma/abokai?

Su wane ne masu sauraron da kake so ka cimma?

Ta yaya za ka tallata ra’ayinka ga masu sauraron da kake so ka cimma?

Ta yaya kake ganin masu sauraronka za su mayar da martani?

# Rufe Haske

## Haske

### Sanar da Ɗalibanka

Muna fatan ka ƙara zurfafa tunanin gaba ɗaya game da kyakkyawar dangantaka, musamman dangane da yanda fasaha ta canza abubuwa. Haka kuma muna so ka yi tunanigame da hanyoyin da za ka ƙarfafawa abokanka guiwa domin su “tsaya” ko kuma su tsaya ma kansu da wasu mutanen a lokacin da suka ga wani abun da ba su gamsu da shi ba ko wani abun da yake cutar da wasu.

### Tambayi Ɗalibanka

Wasu abubuwa ne ka koya?

Wasu ayyuka ne ka fi so? Me yasa?

Wasu ayyuka ne ba ka so? Me yasa?

Ta yaya za ka ɗauki abun da ka koya ko ka yi aiki a kai, sannan ka sanya shi a rayuwarka?

Yaya za ka fayyace abun da ka yi ma abokanka?

Wane abu ne sabo ko mai ban mamaki?

Shin kana da wasu tambayoyin game da kyakkyawar dangantaka ko kuma dangantaka mara kyau?

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.